
Waƙar
Ban Mutu Ba
Daga
Fati Nijar

# SASHEN KOYAR DA HARSUNAN NIJERIYA
# JAMI’AR BAYERO, KANO
***HAU4301: Textual Study of Hausa Oral Song***

Makaxiya : Fati Nijar
Waqar : Fati Nijar
G/Waqa: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

1. Jagora: Ya jama’a ga ni da rai,
: Fati Nijar ban mutu ba, X2
‘Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba. X2

2. Jagora : Nai sallama gare ku dukkan al’uma,
‘Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Waqa nake sai ku saurara kuma,
‘Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Na sanar da ku kan qorafin,
: Da ake ta yi na yi gaba,
‘Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

3. Jagora: Rannan da safe na ji ana tai min waya,
‘Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Wajen sau biyar duk jama’a na tambaya,
‘Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Wai gaske ne Fati Nijar,
: Ta mutu ko ba ta mutu ba,
‘Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

4. Jagora: Sai na ce musu Fati ne ke maggana,
‘Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Ban san irin wannan kalamai qanqana,
‘Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Kui haqquri Allahu in dai yai niyya,
: Ba zai bar ni ba,
‘Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

5. Jagora: Masu faxin haka,
: Wai shin me ta tsare muku?
‘Y/Amshi: Ba ta mutu ba.
Jagora: Ku faxa mana ko kuma laifi tai muku,
‘Y/Amshi: Ba ta mutu ba.
Jagora: Kui wa Allah zancenku ya zama alheri,
: Ba sharri ba,
‘Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

6. Jagora: Ya jama’a ga ni da rai,
: Fati Nijar ban mutu ba,
‘Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

7. Jagora : Wani maqaryacin gari,
: Ya je yana ta faxin haka,
'Y/Amshi : Ba ta mutu ba,
Jagora : Wai yana faxin kabarina shi ma yai haqa,
'Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Qarya kake ga ni da rai,
: Fati Nijar ban mutu ba,
'Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

8. Jagora : Ya jama'a ku dinga zancen alferi,
'Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Ko kui shiru,
: Don kar ma kui sharri,
'Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Wannan magana Annabi ne ya faxa,
: Jama'a ba Binta ba,
'Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

9. Jagora : Roqo nake Allah don Almusxafa,
'Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Dukkan sharri,
: Kadda ka bar shi ya qarfafa,
'Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Ka ije mini kai min abin da mutum,
: Ba zai cuce ni ba,
'Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

10. Jagora: Nai gaisuwa dukkan masoya bai xaya,
'Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: An mun sharri har qasarmu gaba xaya,
'Y/Amshi: Ba ta mutu ba,
Jagora: Ku yi haquri ga ni da rai,
: Fati Nijar ban mutu ba,
'Y/Amshi : Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba.

11. Jagora: Ya jama'a ga ni da rai,
: Fati Nijar ban mutu ba,
'Y/Amshi: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba,
: Ayyaraye ga ta da rai Fati Nijar,
: Ba ta mutu ba,